**EPISODE 9**

**<u>CHARACTERS</u>**

***DR. DAOUD***

***LARABA***

***EZE***

***TANKO***

***TANKO***

***HUSSEINI***

**Episode 9, Scene 1**

**NORTHERN KADUNA. HEALTH CENTER. MORNING**

1. **MUSIC:** **<u>THEME MUSIC</u>**
2. **SFX:** **<u>BUSY HEALTH CENTER AMBIENCE. SOUND OF CHILDREN CRYING. DOOR OPENS AND CLOSES.</u>**
3. **LARABA:** (**BRISKLY)** Ina Kwana, Dacta. Daoud.
4. **DR. DAOUD:** **(CHEERFULLY)** Oh Ina kwana Laraba, yaya keki yau?
5. **LARABA:** Ina lafifa lau Dacta Daoud, ga katin wadannan masu jinyyar
6. **DR. DAOUD:** Yauwa, suna nawa ne anan?
7. **LARABA:** Gaba daya sun kai talatin
8. **DR. DAOUD:** Sun yi yawa ma rana daya, bani in dubu in maida miki wanda zaki iya bitar su.
9. **SFX:** **<u>RUSTLING OF PAPERS.</u>**
10. **LARABA:** Da sauran da dan dama a waje, kilar zan sake kawo maka wasu katin anjima

11. **DR. DAOUD:** Hmm yau akwai aiki, Laraba, amshe wadannan katin ki yi bitar su

12. **LARABA:** Na'am, Likita. (**MAKES TO LEAVE)**

13. **DR. DAOUD:** **(SOLICITIOUSLY)** Nars Laraba. Yaya kike fuskantar wannan asibitin, na tabbata akwai babban ce sosai.

14. **LARABA:** (**CHEERFULLY)** Na soma jin dadin nan wurin Dacta Daoud

15. **DR. DAOUD:** Kina nufin ba kei kewar Zaria?

16. **LARABA:** **(EXCITED)** Ina yi Likita, amma na so ma tsabawa da al'umar na, Jama'ar suna da kirki da fara'a, ji nake kamar ni yar al'umar ne ma.

17. **DR. DAOUD:** **(LAUGHING)** Kin san me, na yarda saboda akwai fara'a a tare da ke lokacin da kike Magana akan al'umar

18. **LARABA:** **(LAUGHING)** Gaskiyan ka Dacta Daoud, ina da burin in taimaka wurin ceton rayuwa a wannan al'umar.

19. **DR. DAOUD:** Nallai, wannan zancen da dadi, amma ina batun mijin ke da yayan ki? Kuna tare anan ne koko…

20. **LARABA:** **(INTERRUPTS)** Bani da aure Dacta Daoud

21. **DR. DAOUD:** **(SURPRISED)** Baki da aure? Abin mamaki kyakyawar nars mai kwazon aiki kuma ba a yi ribibi akan ki ba

22. **LARABA:** Likita, na gamsu da aiki na

23. **DR. DAOUD:** Toh Nars Laraba, nima bani da aure

24. **LARABA:** **(NERVOUS)** Erm Dacta Daoud, bara in je in yi bitar wadan nan kati da ka bani

25. **MUSIC:** **BRIDGE MUSIC.**

**Episode 9, Scene 2**

**Northern Kaduna. Eze's Chemist Shop. Afternon.**

26. **SFX:** **LIGHT TRAFFIC. SOUND OF CLANGING OF METALS.**
27. **TANKO:** Kai Eze. Me kake yi a wurin shagon ka
28. **EZE:** **(CHEERFULLY)** Kai Tanko! Na shari kashin awakin da ke nan ne
29. **TANKO:** **(LAUGHING)** kai da awakin nan, suna yawan son hutu a gefen shagon nan naka
30. **EZE:** Kuma su bar ni da shara ba, yaya kake? Ya sana'a kuma?
31. **TANKO:** Sai godiya Eze, saida har yanzu ina kwankwaso nan a ciwo
32. **EZE:** Ai, kai ka ki kwayar magani mai karfin da naba ka shawara
33. **TANKO:** Ba wain a ki bani ai, ban i da kudin biya ne, ka san fa ban biya raguwar kudin maganin zazzabin ciwon sauro da ka bani ba fa
34. **EZE:** Wato da dukan kudin da kake samu, baza ka iya ka kula da kanka ba? Ka san dai sana'ar na bukatar takawa, kada kayi sakaci da lafiyar ka fa
35. **TANKO:** (**RUSTLING OF MONEY)** Amshe, ga wannan, bara in karasa biyar raguwar kudin maganin zazzabin ciwon sauro da ka bani
36. **EZE:** Tanko Nagode, amma kun hada da sabuwar Nars din nan Laraba kuwa?
37. **TANKO:** E, na hadu da ita, amma tana ta ji da kanta, kilar saboda tasan ita kyakyawa ce.

38. **EZE:** **(LAUGHING)** kana Magana kamar wanda ya nema bai samu ba, ko dai harka gwada nema ni

39. **TANKO:** Toh, bara in gaya maka, idan har zata ci gaba da ji da kanta, toh baza ta taba samun mijin aure ba.

40. **EZE:** Ban yarda da abinda kace game da cewa tana da dagun kai ba, da ta zo nan naga kamar tana da saukin sha'ani kuma ta san aikin ta

41. **TANKO:** **(SURPRISED)** Nars Laraba, tazo nan?

42. **EZE:** E, tazo nan mana, har ta fada min game da kungiyar da take son in zama daya daga cikin mamba ta

43. **TANKO:** Abin mamaki!

44. **EZE:** Me abin mamaki game da hakan? Abin mamaki ne budurwan ta yaba amfani na a al'umar?

45. **TANKO:** Aa, bah aka nake nufi ba fa. Na ji takamammai labara cewa bata son shagon saida magani

46. **EZE:** Tanko, ka dai maganan banza. Ya z aka ce bata son shagon magani bayan it ace ke bi tana son su hada kai wajen shirin Muyi Tare

47. **TANKO:** Toh Eze, bayan ji da kai da wuyan sha'ani, tana kuma da Magana biyu

48. **EZE:** Me kake nufi?

49. **TANKO:** Toh,Laraba da kake yabawa, ta nuna me rashin jin dadi amfani da maganin shagon magani

50. **EZE:** kai! Tanko ka tabbata da abin da kake fada kuwa? Ina fatan ba wai kana fadar haka saboda taki aminci maka bane?

51. **TANKO:** Me yasa, ka yi zaton zan iya muguntar kaga mata karya haka. Ka tabaya ta indan ka hadu da ita, baza ta iya musuntawa ba sai dai idan makaryaciya ce.

52. **EZE:** Idan akwai abin da na tsana shine mutane masu fuska biyu, domin mutum ba zai san takamaamman abinda zai yi indan yana tare da su ba

53. **TANKO:** Yauwa! Eza ka fara gane wace irin mutum ce Nars Laraba ai, ko?

54. **EZE:** **(CONFUSED)** Amma Tanko, yaya za ta ce bata son masu shagon saida magani bayan tana gayattar mun mu kasance cikin kungiyar lafiyar da take son kafawa anan al'umar?

55. **TANKO:** **(MEAN LAUGH)** Amma haka mutanin da ke da fuska biyu keyi ai

56. **EZE:** Tanko, abin nan ya ruda ni fa

57. **TANKO:** Eze, kadai yi hankali da ita, kada kazoo ka rasa abokan cinikin ka

58. **EZE:** Tanko, mutane nada mugunta sosai fa, abin na bani mamaki cewa Nars Laraba tana da fuska biyu

59. **MUSIC:** **BRIDGE MUSIC**

**Episode 9, Scene 3**

**NORTHERN KADUNA. HEALTH CENTRE. AFTERNOON.**

60. **SFX:** **BRISK STEPS. CRYING CHILDREN. DOORS OPENING AND CLOSING.**

61. **JUMMAI:** **(KNOCKING).** Nars Laraba?

62. **LARABA:** **(OFF MIC)** Shigo, mallama Jummai

*63.* **JUMMAI:** **(DOOR OPENS)** Sannunki nars Laraba

64. **LARABA:** yaya kike Mallama Jummai? Lokacin da na fito daga gidan yau nag a kin riga da kin tafi

65. **JUMMAI:** Haka ne nars Laraba, naji in dauko wani abu a wurin aikina kafin na zo nan

66. **LARABA:** da kika zo kwanakin baya kin gaya min kina son ki chanja hanyar tazarar haihuwan da kike amfani dashi yanzu

67. **JUMMAI:** Hakika, mun tattauna da Maigida na, yama so ya zo tare da ne yau amma suna da taro a kungiyar sun a yan kasuwa

68. **LARABA:** Yayi kyau kwarai. Tattaunawa tsakanin Mace da Maigidanta yana da muhimunci sosai, musanman yake shawarar hanyar tazarar haihuwa da za su amfani da shi. Wane shawara kuka dauka?

69. **JUMMAI:** Mun yake shawara amfani da hanyar da zai fi dadewa fiye da alurai, muna tunanin zai rage mana lokacin zuwa dubiya akai akai.

70. **LARABA:** Daidai ne, akwai wanda kuka fi so ne?

71. **JUMMAI:** E, muna son wanda ake sanyawa a kafada

72. **LARABA:** Toh, yayi, amma mallama jummai ko kin san akwai wanda ke jimawa har tsawon shekaru uku akwai kuma na tsawon shekaru biyar?

73. **JUMMAI:** E, mun karanta dan litaffin da kika bamu, kuma mun yi sha'awar wannan na shekaru ukun

74. **LARABA:** Toh, mun gamsu da hanyar kenan, abinda ya saura shine in dan tabbayaki wasu abubuwa mu tabbatar ko wannan hanyar ta dace da ke, ki ma idan kina da tambaya sai ki yi min.

75. **JUMMAI:** **(IMPRESSED)** Nars Laraba, ke kwarariya ce kuma kina da kwazo, sai yasa kowa ki yaba miki

76. **LARABA:** (**TEASING)** Dole in kyauta ma dukan yan gidan da nake tare dasu ai, bayan ma suna yimin kirki?

77. **JUMMAI:** (**LAUGHING)** Amma bani kadai kike kyautawa ba ai, kina kyauta ma dukan jama'ar al'umar nan da suka zo maganar tazarar haihuwa

78. **LARABA:** Kowa nayi kuskure, amma ina farin ciki kuna jin dadin aikina

79. **JUMMAI:** Hakika, muna jin dadin aikin ki, kowa ya yaba da hakurin ki, fara'ar ki, da kuma kwazon ki da kwariwar ki wurin aiki

80. **LARABA:** Wadannnan horo ne da muka samu a lokacin da muke kartun koyan aiki, saboda samar da ingantancin lafiya a duk inda muke da shirin nan na muyi tare

81. **JUMMAI:** Ni dai abin da na sani shine muna farin cikin samun ki a asibitin wannan al'umar tamu

82. **LARABA:** Nagode kwarai mallama jummai, toh bari in dan same Karin bayani gare ki sai mu sanya miki hanyar tazarar haihuna ta.

83. **MUSIC:** **<u>BRIDGE MUSIC</u>**

**Episode 9, Scene 4**

**Northern Kdn. Husseini's Mai Shayi Spot Near The Motor Park.**

84. **SFX:** **<u>BUSY TRAFFIC. CAR HORNS BLARING AND MUSIC PLAYING.</u>**

85. **EZE:** **(COMING ON-MIC)** Abokina, Husseini, nayi murnan ganin ka a rufar ka?

86. **HUSSEINI:** **(ON MIC)** Kai Eze! Barka ka!

87. **EZE:** **(CHEERFULLY)** Yau dai, nace dole in tsaya in ga rufa nan da ake ta Magana akai

88. **HUSSEINI:** **(LAUGHING)** Ake ta Magana akai? Wannan dan rufar tawa, ko dai wani babbar shago kake batu akai

89. **EZE:** (**SHOULDER SLAPPING)** Kada ka damu aboki na, yaro zai girma ai, kada ka ki samuwa kadan kadan, nay i farin ciki da rufar a yanzu.

90. **HUSSEINI:** Nagode Eze, ka karfafa ne ai

91. **EZE:** Maganar gaskiya, sabuwar rufa da duk kayan nan, ai aciki take Husseini.

92. **HUSSEINI:** Dukan wannan fa taimakon Alhaji Bature ne da a bani damar amsar kaya a bashi in dinga biya bayan nay i ciniki

93. **EZE:** Ya kyauta, ina fatan mutane baza su yi maka makirchi, su hada kanku da Alhaji ba, har ta kai yak i baka kaya

94. **HUSSEINI:** Amma Eze, kana ganin akwai wanda zai son yi haka ne? Ba ruwa na da harkan kowa.

95. **EZE:** baza ka gane ma irin mutanan masu fuska biyu ba ai

96. **HUSSEINI:** Menene ya faru Eze? Me kake fada ne? Wani abu mara dadi ya faru kenan ai, menene ya faru

97. **EZE:** **(DEEP SIGH)** Tanko ne ya fada min game da munafikan nan wanda ake kira Nars Laraba.

98. **HUSSEINI:** (**SURPRISED)** Munafika? Nars Laraba ce munafika? Me kake fada ne?

99. **EZE:** Tanko, Kana jin cewa, ta hana shi amfani da maganin shagon magani kuma ta bashi shawarar kada ya sake zuwa shagon magani

100. **HUSSEINI:** Kai gaskiya ne kuwa? Amma Eze kai da kanka ka fada min cewa ta gayace ka zama mambar kungiyar lafiyan al'umar da take nufin kafawa

101. **EZE:** E amma, ta zaga tana gaya ma jama'a kada su yi sayaya a shago na

102. **HUSSEINI:** Ina ganin ta kamar mutuniyar kirki, mai gaskiya da rikon amana, ka san a cikin gidan mu take da zama

103. **EZE:** Ina ganin fuska biyu gare ta, ku dai yi hankali da ita abokina

104. **HUSSEINI:** Kai, bana son in yarda da abin nan game da Nars Laraba. Na tabbata rashin fahimta ne kawai Eze. .

105. **EZE:** Kada dai kace baka sani ba lokacin da ta gwada maka ainihin halin ta

106. **HUSSEINI:** Tana kama da masu kirki sosai, kuma tana da ladabi ma

107. **EZE:** **(SCOFFS)** Hmm Husseini… ladabi?! Duk abinda take yi kamar sune halayenta karyane, babbar munafika ce

108. **MUSIC:** <u>**THEME MUSIC**</u>